Kuji kuma Kub,i koda kuwa kuwa Bawa Bahabashe aka Shugabantar muku, Kai kace kansa gudaddajin Zabibi ne

An rawaito daga Anas Bn Malik -Allah ya yarda da shi- Manzon Allah SAW ya ce:"Kuji kuma Kub,i koda kuwa kuwa Bawa Bahabashe aka Shugabantar muku, Kai kace kansa gudaddajin Zabibi ne"

[Ingantacce ne] [Buhari ne ya rawaito shi]

Ku laimci Ji da biyayya ga Shuwagabannni, kuma koda Za'a dora muku Bawa Bahabashe -na Asali ko ko reshensa ko kuma a Halitta- a kan ku, wanda gashin Kansa Kamar zabibi, kuma wannan an fada ne ta hanyar kanbamawa cikin kasancewar wannan Ma'akacin Bawa ne bahabashe na Asali ko wani reshi daga shi, fadinsa: "Koda za'a dora muku" ya hade Shigaban da yake karbar Umarni daga Sarki, haka ma in shi ne Sarkin, da ace cewa Sarki ya yaki mutane yai Nasara a kansu kuma koda ba Balarabe ba ne; kai ace ma Bawa ne daga Habasha, to ya wajaba mu ji kuma mu bi shi, to wannan Hadisin yana nuna Wajabcin biyayya ga Shuwagabannni sai in Sabon Allah ne, saboda Alkairan da Zaman Lafiya da kwanciyar Hankalin dake cikin sa, da rashin tashin Hankali da rashin bin Son rai amma idan aka sabawa shuwagabanni cikin wani Al-amari da ya Wajabata ayi musu biyayya a cikinsa; saboda za'a iya samun tashin tashina, kuma za'a kowa ya kafe kan Ra'ayinsa, sai a rasa zaman lafiya, kuma abubuwa su baci, kuma futuntunu suyi yawa.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6382